# DOKAR

# KULA DA LAFIYAR MATA DA ƘANANAN YARA KYAUTA TA JIHAR KANO

## 2023
## (1444 A.H)

RESOURCE CENTRE FOR HUMAN RIGHTS & CIVIC EDUCATION (CHRICED)

# DOKAR KULA DA LAFIYAR MATA DA KANANAN YARA KYAUTA TA JIHAR KANO 2023 (1444 A.H.)

# DOKAR DA ZA TA SAMAR DA KULAWA KYAUTA GA MATA DA KANANAN YARA A JIHAR DA KUMA AL'AMURAN DA SUKA SHAFI HAKA.

Majalisar Dokokin Jihar Kano ta amince kamar haka:

| | | |
|---|---|---|
| **Tsakure da Lokacin Aiwatarwa** | 1. | Za a iya kiran wannan doka Dokar kula da lafiyar Mata da Ƙananan yara Kyauta ta Jihar Kano, 2023 (1444 A.H) kuma za ta fara aiki ranar 10 ga watan Mayun 2023 (1444 A.H). |
| **Bayani** | 2. | A wannan dokar, sai dai idan bayani ya buƙaci saɓanin haka:<br><br>**"Zuwa Awo"** ya ƙunshi gano cikin, da zuwa yin gwaje-gwaje a kai a kai, dubawa da kula da wata matsala yayin da mace take da juna biyu;<br><br>**"Yaro"** na nufin jariri zuwa ɗan wata 59. |

**"Gwamnatoci"** na nufin gwamnatin jihar Kano da ta ƙananan hukumomin jihar.

**"Mai bayar da kulawa",** game da yaron ya haɗa da wanda, a ra'ayin kotu, yake da wata alaƙa da yaron ko abin da ya shafi yaron wanda yake kula ko kuma tafiyar da al'amuran yaron na tsawon lokaci;

**"Samun izini"** na nufin izinin da aka samu daga mara lafiya ko iyaye ko mai kula da shi ko wani ɗan'uwa cikin sauƙi ba tare da barazana, yaudara ko amfani da hanyar da ba ta dace ba, bayan samun isassun bayanai a harshen da mara lafiya ko iyaye ko mai ba da kulawa ko ɗan'uwa ya fahimta;

**"Daukan mataki bayan samun bayanai"** na nufin zaɓin da mara lafiya ya ɗauka na amfani ko ƙin amfani da tsarin iyali ko sauran

matakan tsara haihuwar yara bayan samun isassun bayanai dangane da alfanu da illolin dukkanin hanyoyin;

**"Kula da Lafiyar mai juna biyu"** na nufin kula da lafiyar mace yayin da take da ciki da lokacin haihuwa har zuwa kwana arba'in da biyu bayan haihuwa;

**"Asibitin kula da masu juna biyu"** na nufin duk asibitin da gwamnati ta ware, hukumomi suka bai wa izinin kula da mata da ƙananan yara kyauta;

**"Masu kula da lafiyar mata"** na nufin duk wani mutum ko wata cibiya da doka ta sahhalewa su kula da lafiyar mata da ƙananan yara;

**"Likita"** na nufin duk wani mutum da yake da shaidar zama likita daga ƙungiyar likitoci ta Najeriya bisa tanadin dokar

aikin likita ta Najeriya mai lamba ta Cap M8 na dokokin Tarayyar Najeriya ta 2004;

**"Malaman jinya da Ungozoma"** na nufin mutumin da yake da cikakkiyar rajista a matsayin malamin jinya ko ungozoma a ƙarƙashin Dokar ma'aikatan jinya da ungozoma lamba ta Cap N143, na dokokin Tarayyar Najeriya, 2004;

**"Juna biyu"** na nufin samun ɗan tayi a ciki mahaifa.

**"Kulawar bayan haihuwa"** na nufin ci gaba da ganin likita da bai wa uwa da jaririnta magani.

**"Lafiyar Mahaifa"** na nufin tabbatar da lafiyar mahaifa ba wai kawai rashin ganin wata cuta ba;

| | | |
|---|---|---|
| | | **"Ƴancin samun bayanan da suka shafi haihuwa da reno"** na nufin ƴancin samun bayanai da bai wa mata ingantacciyar kulawa daga lokacin da suke da ciki har zuwa haihuwa da nufin tabbatar da lafiyar uwa da jariri;<br><br>**"Zubar da ciki"** na nufin bin tsarin likita wajen zubar da ciki kafin ɗan tayi ya iya rayuwa a wajen mahaifa. |
| **Dalilai da Manufa** | 3. | Dalilai da manufar wannan dokar su ne-<br>(a) A samu raguwar mace-macen mata masu juna biyu da yara a jihar Kano.<br><br>(b) Samar da tsarin shari'a don bunƙasa lafiyar mata masu juna biyu da yara da reno da kuma kula da lafiyar yara.<br><br>(c) Tabbatar da samar da ingantacciyar kulawar da ta |

| | | |
|---|---|---|
| | | dace ga mata masu juna biyu da ƙananan yara a jihar Kano. |
| **Kula da lafiyar mata da kananan yara kyauta** | 4. | (1) Daga fara aiwatar da wannan doka, gwamnatin jihar Kano hadin gwiwa da gwamnatocin ƙananan hukumomi za su samar da kuɗi na kula da lafiyar mata da ƙananan yara kyauta a jihar Kano.<br><br>(2) Samar da kuɗin sayen magani da magungunan inganta lafiyar mai juna biyu da kayan gwaje-gwaje na kula da lafiyar mace mai juna biyu da jariri da ƙananan yaran da ba su wuce shekara biyar ba.<br><br>(3) Samun damar amfani da kashi bakwai cikin 100 daga kashi 10 cikin 100 na kuɗin da aka ware don kula da lafiyar mata da ƙananan yara |

a Dokar Asusun Tallafawa Lafiya ta Jihar Kano don hidimar kula da lafiyar uwa da ƙananan yara a ƙarkashin wannan doka.

(4) Ɓa tare da illa ga tanadin sashe na 3 na dokar hukumar bunƙasa lafiya a matakin farko ba, lamba ta Cap N2 na dokokin tarayyar Najeriya 2004 Gwamnatoci za su ware aƙalla:

(a) asibiti guda na kula da lafiyar mata da ƙananan yara a dukkanin hedikwatar ƙananan hukumomi;

(b) ɗaya cikin asibitocin a kowane gari ko ƙauye da bai wuce tazarar kilomita 10 ba daga cibiyar wata ƙaramar hukuma ko daga wata cibiyar kula da lafiyar mata.

(5) Ayyukan kula da lafiyar mata kyauta da za a samar za su ƙunshi amma ba su taƙaita ga waɗannan ba:

(a) kulawa kyauta lokacin awo da sauran laulayi yayin da mace take da juna biyu har da gwaje-gwaje akai akai da duba lafiyarta da kuma ba ta magunguna.

(b) Bai wa mata masu juna biyu damar samun kulawa a kan lokaci yadda ta kamata a lokacin awo ba tare da duba matakin matsala ba na tsawon shekara ɗaya.

(c) Kula da lafiyar jariri da ƙananan yara ƴan ƙasa da shekara biyar kyauta.

(d) ba da kulawa kyauta a lokacin haihuwa.

(e) Yin tiyatar ciro jariri kyauta (ko bisa zaɓin mace ko kuma tiyatar gaggawa).

(f) Zubar da cikin da ke wajen mahaifa a kyauta.

(g) ba da kulawa kyauta ga wata matsala ta haihuwa da ta taso.

(h) samar da motar ɗaukan mara lafiya kyauta kuma a sauƙaƙe ta hanyar haɗin guiwa da al'umma.

(i) Kulawa kyauta ga uwa da jariri bayan haihuwa.

(j) Samar da maganin cututtukan da ke yaɗuwa ta hanyar saduwa.

| | | |
|---|---|---|
| | | (k) Bayar da kulawa ga macen da ta haihu har da kula da ciwo ta sanadiyyar cin zarafi a gida.<br><br>(l) Samar da duk kulawar da ta kamata ba tare da duba yanayin matsala ba, ga jariri da yara na tsawon shekara ɗaya zuwa wata 59.<br><br>(m) Samar da ingantattun dabarun kula da cututtukan yara da duk wasu matsaloli. |
| **Masu kula da lafiyar mata masu juna biyu da kananan yara** | 5. | (1) Waɗanda za su kula da lafiyar mata masu juna biyu da ƙananan yara sun haɗa da:<br>(a) Likita;<br>(b) Malaman Jinya;<br>(c) Unguwar zoma<br>(d) Kwararrun ma'aikatan lafiya; da |

| | | |
|---|---|---|
| | | (e) Ma'aikatan kula da Lafiyar al'umma.<br><br>(2) Gwamnatocin za su tanadar wa masu kula da lafiyar mata da ƙananan yara wadatattun kayan aikin kula da lafiya. |
| **Tazara da lokacin haihuwa** | 6. | (1) Gwamnatoci za su samar da isassun ma'aikata da wuraren wayar da kai da bayar da shawarwari game da tazarar iyali da lokacin haihuwa.<br><br>(2) Dole ne masu kula da lafiyar mata masu juna biyu da ƙananan yara su fahimtar da mutumin da ƙaramin sashe na 1 na wannan sashen ya shafa, alfanu da rashin alfanun ƙayyade lokacin haihuwa da tazarar iyali, domin samun amincewar wannan mutumin, kafin rubuta tsarin tazarar |

haihuwa da ya fi dacewa da shi.

(3) Mutumin da wannan sashe ya shafa yana da ƴancin samun ayyukan da aka ambata a sama da duka sauran abubuwan da suka dace da suka shafi tsarin da aka zaɓa, a kyauta.

(4) Bai kamata masu kula da mata masu juna biyu da ƙananan yara ko wani mutum da ke da bayanan da aka zayyana a ƙaramin sashe na (1) na wannan sashe ya yaɗa bayanin ga wani ba sai dai bisa yadda wannan dokar ta tanada.

(5) Mutumin da ya saɓa tanadin ƙaramin sashe na (4) na wannan sashe ya aikata laifi kuma ana iya cin shi tarar da ba ta wuce N100,000 ba ko kuma hukuncin zaman

| | | |
|---|---|---|
| | | gidan yari na lokacin da bai wuce shekara ɗaya ba ko kuma duka biyu. |
| **Kulawa a lokacin awo** | 7. | Duk wani asibiti da aka ware don kula da lafiyar mata da ƙananan yara zai samar da kulawa lokacin awo kyauta wanda zai haɗa da mata masu juna biyu zuwa ganin likita akai akai. |
| **Taimaka wa mace yayin haihuwa** | 8. | (1) Za a samar da isassu da kuma lafiyayyun kayan aiki don amfani wajen taimakon mace ta haihu da kanta ta hanyar amfani da dabarun ciro jariri a kowane asibiti da aka ware na kula da lafiyar mata masu juna biyu da ƙananan yara da nufin taimaka wa mace ta haihu kyauta.<br><br>(2) Ya kamata gwamnatoci su ɗauki ƙwararrun jami'an kula da lafiyar mata da ƙananan yara aiki a dukkan |

| | | |
|---|---|---|
| | | asibitocin da aka ware da za su iya amfani da kayan aikin da aka ambata a ƙaramin sashe na 1. |
| **Tiyatar ciro jariri** | 9. | (1) A duk lokacin da likita yake tunanin mace mai ciki ba za ta iya haihuwa da kanta ba, yana iya ba da shawarar a yi tiyatar ciro jariri.<br><br>(2) Za a yi wa mai juna biyun da likita ya ba da shawarar a yi mata tiyata kyauta.<br><br>(3) Gwamnatoci za su samar da isassu kuma ingantattun kayan aiki da ƙwararrun masu kula da lafiyar mata masu juna biyu da ƙananan yara a dukkan asibitocin kula da lafiyarsu don yi wa mai juna biyu tiyata. |
| **Ciki a wajen mahaifa** | 10. | (1) Shi ne idan likita ya gano cewa cikin da mace ke ɗauke |

| | | |
|---|---|---|
| | | da shi yana wajen mahaifa, wannan juna biyun na buƙatar kulawar likta.<br><br>(2) Zai zama nauyin gwamnati ta samar da isassu da ƙwararrun masu kula da lafiyar mata masu juna biyu a dukkan asibitocin da aka ware domin tabbatar da an kula da cikin da ke wajen mahaifa da aka ambata a ƙaramin sashe na (1) wanda ya haɗa da aiwatar da sashe na 11 na wannan doka. |
| **Zubar da ciki** | 11 | (1) Ana iya zub da ciki idan bayan yin magana da mai juna biyu likita ya ce –<br>(a) Zai yi wuya a iya kula da cikin da ke wajen mahaifa: ko<br><br>(b) Kyale cikin zai iya jefa rayuwar uwar a cikin haɗari; ko |

(c) Lafiyar uwar na cikin haɗari sanadiyyar cikin da take ɗauke da shi.

Matuƙar likitan zai ba da shawarwari ba na dole ba sannan ba umarni ba, kafin da kuma bayan an zubar da cikin.

(2) dangane da sashe na 11 (1), za a zubar da cikin –

(a) da amincewar mai juna biyun kaɗai;

(b) idan ƙaramar yarinya ce ke ɗauke da juna biyun ko kuma mai rangwamin hankali, bayan tuntuɓar iyayensu, ko mai kula da su, amma a kowane yanayi, za a bi buƙatarsu ne.

(c) idan yanayin na gaggawa ne bayan tuntuɓar mijin

| | | |
|---|---|---|
| | | ko wani ɗan'uwan mai juna biyun. |
| **Motar daukan mara lafiya** | 12. | (1) Za a samu motar ɗaukan mara lafiya aƙalla guda ɗaya da ta dace da gari ko ƙauyen a dukkan asibitocin kula da lafiyar mata da ƙananan yara da aka keɓe wanda al'umma za ta yi aiki a ƙarƙashin jagorancin shugabansu.<br><br>(2) Motocin ɗaukan mara lafiya za su yi aiki kyauta ga mata masu juna biyu da matan da suka kusa haihuwa a cikin yankin da ke wurin asibitin kula da lafiyar mata masu juna biyu inda aka ajiye motar ɗaukan mara lafiyan. |
| **Kula da mace da jaririnta bayan haihuwa** | 13. | (1) Kowane asibitin kula da mata masu juna biyu da aka keɓe zai samar da:-<br>(a) Kulawa ga uwa bayan haihuwa kyauta har tsawon mako shida. |

| | | |
|---|---|---|
| | | (b) Kulawa ga jariri kyauta har zuwa wata 59 bayan haihuwa.<br><br>(2) Kulawa kyauta za ta ƙunshi:-<br>(a) Duba lafiyar uwa da ɗanta ko ƴaƴanta akai akai;<br><br>(b) Bai wa uwa da ɗanta ko ƴaƴanta magani kyauta bayan haihuwa. |
| **Kafa hukumar tuntuɓa** | 14. | (1) Za a kafa wannan hukuma a ƙarƙashin kulawar Ma'aikatar Kuɗi da Tsare-Tsare da za a riƙa kira "Hukumar Tuntuɓa kan lafiyar mata masu juna biyu da ƙananan yara kyauta" (a wannan dokar ana kiranta "hukuma") domin aiwatarwa da kuma sa ido kan wannan doka a jihar Kano. |

| | | |
|---|---|---|
| | | (2) Hukumar;-<br>(a) za ta ci gaba da aiki ko da an samu giɓi na shugabanci da kuma hatimi ɗauke da sunan hukumar;<br><br>(b) za ta iya shigar da ƙara ko a shigar da ita a sunanta, da<br><br>(c) za ta iya mallaka ko riƙe ko ma watsar da duk wasu kaya ko fili don aiwatar da ayyukanta a ƙarƙashin wannan dokar, da amincewar gwamna. |
| **Ayyukan hukumar** | 15. | Hukumar za ta ɗauki nauyin gudanarwa da kula da asusun da aka ware don samar da kulawa kyauta ga mata masu juna biyu a jihar Kano da ɗaukacin ƙananan hukumomi. |

| | | |
|---|---|---|
| **Naɗi da tsarin hukumar** | 16. | Mambobin hukumar za su kasance bisa naɗin gwamna amma sai majalisar dokokin jihar ta tabbatar da naɗin sannan za ta ƙunshi:-<br>(a) Shugaba wanda zai;-<br>(i) Mutum mai nagarta da ƙwarewa da kuma ilimin tafiyar da harkar lafiya, da<br>(ii) Samun cancanta da ƙwarewar da ake buƙata wajen aiwatar da ayyukan wannan ofishin; da<br><br>(b) Mutum uku, mutum ɗaya daga kowace shiyya a mazaɓun majalisar dattawa a jihar;<br><br>(c) Wakili daga duk ma'aikatun jihar waɗanda muƙaminsu ya kai na darakta:-<br>(i) Lafiya |

| | | |
|---|---|---|
| | | (ii) Kuɗi,<br>(iii) Harkokin mata,<br>(iv) Shari'a, da<br>(v) Ƙananan hukumomi.<br>(d) Wakili ɗaya daga ƙungiyoyin farar hula<br><br>(e) Wakilai biyu daga hukumomin kula da lafiya |
| **Wa'adin aiki na ma'aikatan hukumar** | 17. | Ma'aikatan hukumar ban da mambobi shida na hukumar gudanarwa za su riƙe muƙami na tsawon shekara huɗu a matakin farko kuma wataƙila zai iya samun damar ƙara wasu shekarun huɗu amma ba zai wuce haka ba; |
| **Albashin ma'aikatan hukumar** | 18. | Ma'aikatan hukumar za su samu albashin da gwamna lokaci zuwa lokaci ya yanke. |
| **Hanyoyin samun kuɗaɗe** | 19. | Kuɗaɗen gudanar da wannan dokar za su ƙunshi:<br>(1) Kasafin kuɗi |

(2) Tallafi daga gwamnati

(3) Kuɗin da aka ware wa asusun kula da lafiya na jihar Kano; da

(4) Tallafi daga abokan hulɗa da masu ba da tallafi.

Matuƙar ƙa'idojin tallafin da kyaututtukan ko alkawarurruka ba su ci karo da tanadin wannan doka ba.

# SA-HANNUN MAGATAKARDAN MAJALISAR DOKOKI

NA YI NAZARIN BAYANIN DA AKA BUGA DA **KUDIRIN KULA DA LAFIYAR MATA MASU JUNA BIYU DA KANANAN YARA TA JIHAR KANO TA SHEKARAR 2023 (1444 BAYAN HIJIRA)** WANDA MAJALISAR DOKOKIN JIHA TA AMINCE DA SHI SANNAN NA TABBATAR DA SAHIHANCIN KWAFIN WANNAN DOKA DA AKE MAGANA A KAN TA

……………………………………………………

**GARBA BAKO GEZAWA**
**MAGATAKARDA/SHUGABAN HUKUMAR KULA DA AYYUKAN MAJALISAR DOKOKIN JIHAR KANO**

NA AMINCE DA WANNAN:

20th GA WATAN Shawwal 1444 BAYAN HIJIRA

10th GA WATAN May 2023

**DR. ABDULLAHI UMAR GANDUJE (OFR)**
**MAI GIRMA GWAMNA**
**JIHAR KANO**